HA



# *Zanen ’yan yatsu da kuma rumbun adana zanen hannu na Tarayyar Turai*

**Bayani bisa ga Mataki na 29 (3) na Dokar (Tarayyar Turai) Lamba 603/2013 don ‘yan wasu ƙasashe ko mutanen da ba su da ƙasa da suke zaune ba bisa izini ba a wata ƙasa da take mambar Tarayyar Turai**

Idan kana zaune ba bisa izini ba a cikin wata ƙasar Dublin [1], mahukunta za su iya ɗaukar zanen yatsunka da kuma tura su zuwa rumbun adana bayanan zanen yatsa na 'Tarayyar Turai'. Maƙasudin wannan shi ne don fayyace ko ka riga ka nemi mafaka. Ba za a ajiye bayanan yatsanka a cikin rumbun adana bayanai na Tarayyar Turai ba, amma, idan ka riga ka nemi mafaka a wata ƙasa, za a iya mayar da kai zuwa wannan ƙasa.

Idan zanen yatsunka ba su da inganci sosai, misali idan da gangan ka ɓata su, to, za a sake ɗaukar zanen yatsun naka daga baya.

Wata hukumar Tarayyar Turai mai suna eu-LISA ita ce take kula da Rumbun Adana Bayanai na Tarayyar Turai. Ta yiwu a yi amfani bayananka don dalilai da doka ta bayyana. Na'urar cibiyar Rumbun Adana Bayanai na Tarayyar Turai ne yake karɓar bayananka. Idan ka miƙa wata takardar neman a wata ƙasar Dublin a gaba, haka nan za a ɗauki zanen yatsunka don turawa zuwa Rumbun Adana Bayanai na Tarayyar Turai. Ba za a yi musayar bayanan da aka adana a rumbun adana bayanai na Tarayyar Turai da wasu ƙasashe ko ƙungiyoyi da ba na ƙasashen Dublin ba.

1) Ya shafi ɗaukacin Tarayyar Turai (Austria, Belgium, Bulgaria, Croatia, Cyprus, Czech Republic, Denmark, Estonia, Finland, France, Germany, Greece, Hungary, Ireland, Italy, Latvia, Lithuania, Luxembourg, Malta, Netherlands, Poland, Portugal, Romania, Slovakia, Slovenia, Spain, Sweden, United Kingdom) da kuma ƙasashe guda huɗu da suke 'haɗe' na Dokar Dublin (Norway, Iceland, Switzerland and Liechtenstein).

©Tarayyar Turai 2014
An bayar da izinin sake samarwa. Za a sami izinin amfani ko samar da kwafin ɗaiɗaikun hotuna ne kai tsaye daga mamallaka hakkin mallakar.



## Cikakkun bayanan tuntuɓa

**Adireshi da cikakken bayanin hukumar 'yan gudun hijira**
Bundesamt für Migration und Flüchtlinge (BAMF)
Frankenstraße 210
90461 Nürnberg
Tarho.: +49 (0)911 943 0
Fas: +49 (0)911 943 10000
Imel: service@bamf.bund.de

**Adireshi da cikakkun bayanan mai jarrabawar Rumbun Adana Bayanai na Tarayyar Turai**
Bundeskriminalamt (BKA)
65173 Wiesbaden
Tarho.: +49 (0)611 55 0
Fas: +49 (0)611 55 12141
www.bka.de

**Idan mahukuntanmu suka zargi cewa ka miƙa buƙatar neman mafaka a wata ƙasa da kuma cewa wata ƙasa ce take da alhakin manazartar takardarka ta neman mafaka, za su samar maka da karin cikakken bayani game da hanyar da kuma sauran hanyoyi na gaba da yadda za su shafe ka da kuma hakkokinka.**

